Littattafan da Aka Ɗauko Bayanai Daga Cikinsu a *Littafin Taro don Rayuwa ta Kirista da Hidimarmu*

2-8 GA JANAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 2 SARAKUNA 22-23

"Me Ya Sa Zai Dace Mu Zama Masu Tawali'u?"

***lfb* 134 sakin layi na 2**
Josiah Yana Son Dokar Allah

Wani babban firist mai suna Hilkiya ya samo littafin da ke ɗauke da dokar Jehobah a cikin haikalin. Wataƙila wanda Musa ya rubuta da kansa ne. Sai sakataren sarkin mai suna Shaphan ya kawo wa Josiah littafin kuma ya karanta da babbar murya. Da Josiah ya saurari karatun, sai ya gane cewa mutanen sun yi shekaru da yawa suna yin abin da Jehobah ba ya so. Sai Josiah ya gaya wa Hilkiya cewa: 'Jehobah yana fushi da mu. Ka je ka tambaye shi abin da za mu yi.' Sai Jehobah ya gaya wa wata annabiya mai suna Huldah cewa: 'Yahudawa sun daina bauta mini. Zan yi musu horo, amma tun da Josiah bai yi girman kai ba, hakan ba zai faru a lokacinsa ba.'

***w09* 6/15 10 sakin layi na 20**
Ka Kasance Da Himma Don Bautar Jehobah!

A lokacin aikin sake gini da Sarki Josiah ya tsara, Babban Firist Hilkiah ya samu "litafin shari'ar Ubangiji, wanda Musa ya bayas." Sai ya miƙa littafin ga Shaphan, wanda shi ne sakatare sarki, kuma ya soma karanta abin da ke ciki ga Josiah. (*Karanta* 2 *Labarbaru 34:14-18.*) Menene sakamakon? Nan da nan sarkin ya yayyage tufafinsa yana makoki kuma ya umurci mutanen su je su tuntuɓi Jehobah. Ta wurin annabiya Huldah, Allah ya ba da saƙo da ya la'anta wasu ayyukan addinai da ake yi a Yahuda. Duk da haka, an lura da ƙokarce-ƙokarcen Josiah na kawar da ayyukan bautar gumaka, kuma ya kasance cikin tagomashin Jehobah duk da masifu da aka annabta za su faɗa wa al'ummar gabaki ɗaya. (2 Laba. 34:19-28) Menene za mu iya koya daga wannan? Babu shakka muna da muradi irin na Josiah. Ya kamata mu bi ja-gorar Jehobah nan da nan, kuma mu yi tunanin abin da zai iya faruwa idan muka ƙyale ridda da rashin aminci su hana mu bauta wa Jehobah. Kuma za mu kasance da tabbaci cewa Jehobah zai amince da himmarmu don bauta ta gaskiya, kamar yadda ya yi da Josiah.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

***yc* darasi na 8 sakin layi na 1-3**
Josiah Ya Yi Abokan Kirki

Kana ganin yana da sauƙi mutum ya yi abin da ya dace?—Mutane da yawa suna ganin bai da sauƙi. Akwai wani yaro mai suna Josiah, kuma Littafi Mai Tsarki ya gaya mana cewa bai kasance masa da sauƙi ya yi abin da ya dace ba. Amma abokan kirki da yake da su sun taimaka masa. A yanzu za mu ƙara koya game da shi da abokansa.

Amon ne baban Josiah, kuma shi ne sarkin Yahuda. Amon mugu ne kuma ya bauta wa gumaka. Sa'ad da baban Josiah ya mutu, sai Josiah ya zama sarkin Yahuda. Amma shekarunsa takwas ne kawai! Kana ganin shi mugu ne kamar babansa?—A'a.

Josiah yana so ya yi wa Jehobah biyayya tun yana ƙarami. Saboda haka, ya zaɓi mutanen da suke ƙaunar Jehobah ne kaɗai su zama abokansa. Kuma sun taimaki Josiah ya yi abin da ya dace. Su wane ne wasu daga cikin abokan Josiah?

9-15 GA JANAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 2 SARAKUNA 24-25

"Ka Riƙa Tuna Cewa Karshe Ya Yi Kusa"

***w01* 3/1 4 sakin layi na 2**
Ranar Shari'a Ta Jehovah Ta Gabato!

2 Babu shakka annabci da Zafaniya ya yi ya sa Sarki Yosiya matashi ya fahimci bukatar kawar da sujjada mara tsabta daga Yahuza. Amma ayyukan sarkin na kawar da addinin ƙarya daga ƙasar bai share dukan mugunta da ke tsakanin mutanen ba ko kuma ya yi kafarar zunuban kakansa, Sarki Manassa, wanda ya "cika Urushalima da jinin marasa laifi." (2 Sarakuna 24:3, 4; 2 Tarihi 34:3) Saboda haka, ranar shari'a ta Jehovah lalle za ta zo.

***w07* 4/1 10 sakin layi na 11**
Darussa Daga Littafin Irmiya

A shekara ta 607 K.Z., Zedekiah yana shekara ta 11 na sarautarsa. Sarki Nebukadnezzar na Babila ya kewaye Urushalima tun watanni 18 da suka wuce. A rana ta bakwai a cikin wata na biyar cikin shekara goma sha tara na sarautar Nebukadnezzar, Nebuzaradan shugaban matsara "ya zo" Urushalima. (2 Sarakuna 25:8) Wataƙila daga sansaninsa da ke gaban ganuwar birnin, Nebuzaradan ya bincika yanayin kuma ya shirya abin da zai yi. Kwana uku bayan haka, a cikin rana ta goma ga watan, "ya zo" ko kuma ya shiga Urushalima. Kuma ya ƙone birnin.—Irmiya 52:12, 13.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

***w05* 8/1 31 sakin layi na 1**
Darussa Daga Littafin Sarakuna na Biyu

24:3, 4. Domin alhakin jini na Manassa, Jehobah bai 'gafarta' wa Yahuza ba. Allah yana daraja jinin marasa laifi. Mu tabbata cewa Jehobah zai ɗauki fansa domin jinin marasa laifi ta wajen halaka waɗanda suke da hakkin zubar da su.—Zabura 37:9-11; 145:20.

16-22 GA JANAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 1 TARIHI 1-3

"Abin da Ke Littafi Mai Tsarki Gaskiya Ne, ba Tatsuniya Ba"

***w09*-E 9/1 14 sakin layi na 1**
Adam and Eve—Were They Real People?

Consider, for example, the Jewish ancestral lists recorded in the Bible book of First Chronicles chapters 1 to 9 and in the Gospel of Luke chapter 3. These remarkably detailed genealogical records span 48 and 75 generations respectively. Luke traces the genealogy of Jesus Christ, while Chronicles records the royal and priestly ancestral lines for the nation of Israel. Both lists include the names of such well-known figures as Solomon, David, Jacob, Isaac, Abraham, Noah, and finally Adam. All the names in the two lists represent *real* people, and Adam was the original *real* person on each list.

***w08*-E 6/1 3 sakin layi na 4**
Noah and the Flood—Fact, Not Fiction

Two genealogical accounts in the Bible testify that Noah was a real person. (1 Chronicles 1:4; Luke 3:36) Both Ezra and Luke, who compiled these genealogies, were careful researchers. Luke traced Jesus Christ's lineage to Noah.

***w09*-E 9/1 14-15**
Adam and Eve—Were They Real People?

Consider, for example, a Bible doctrine dear to the heart of most churchgoers—the

ransom. According to this teaching, Jesus Christ gave his perfect human life as a ransom to save people from their sins. (Matthew 20:28; John 3:16) As we know, a ransom is a payment of a corresponding value to redeem or buy back something lost or forfeited. That is why the Bible describes Jesus as "a corresponding ransom." (1 Timothy 2:6) Corresponding to what, we might ask? The Bible answers: "Just as in Adam all are dying, so also in the Christ all will be made alive." (1 Corinthians 15:22) The perfect life that Jesus sacrificed to redeem obedient mankind corresponds to the perfect life that Adam lost as a result of the original sin in Eden. (Romans 5:12) Clearly, if Adam did not exist, Christ's ransom sacrifice would be rendered completely meaningless.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

***it*-1-E 911 sakin layi na 3-4**
Genealogy

Names of Women. Women were named in the genealogical registers occasionally when there was a historical reason to do so. At Genesis 11:29, 30, Sarai (Sarah) is mentioned, evidently for the reason that the promised Seed was to come through her, not through another wife of Abraham. Milcah may have been named in the same passage because she was the grandmother of Rebekah, Isaac's wife, thereby showing Rebekah's lineage as being from Abraham's relatives, since Isaac was not to have a wife from the other nations. (Ge 22:20-23; 24:2-4) At Genesis 25:1, the name of Abraham's later wife Keturah is given. This shows that Abraham married again after Sarah died and that his reproductive powers were still alive more than 40 years after their miraculous renewal by Jehovah. (Ro 4:19; Ge 24:67; 25:20) Also, it reveals the relationship of Midian and other Arabian tribes to Israel.

Leah, Rachel, and Jacob's concubines, together with the sons they bore, are named. (Ge 35:21-26) This helps us to understand God's later dealings with these sons. For similar reasons we find the names of other women in the genealogical registers. When an inheritance was transmitted through them, their names might be included. (Nu 26:33) Of course, Tamar, Rahab, and Ruth are outstanding. In each case, there is something remarkable about the manner in which these women came to be in the line of ancestry of the Messiah, Jesus Christ. (Ge 38; Ru 1:3-5; 4:13-15; Mt 1:1-5) Among other instances of the mention of women in the genealogical lists are 1 Chronicles 2:35, 48, 49; 3:1-3, 5.

23-29 GA JANAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 1 TARIHI 4-6

"Mene ne Addu'o'inmu Suke Nunawa Game da Mu?"

***w11* 1/1 10 sakin layi na 3-7**
"Mai-Jin Addu'a"

Jabez mutumi ne mai yin addu'a. Ya soma add'uarsa ne da neman albarkar Allah. Ya roƙi abubuwa guda uku da suka nuna cewa yana da bangaskiya sosai.

Na farko, Jabez ya roƙi Allah, yana cewa: "Ka yalwatadda rabona." (Aya ta 10) Wannan mutumin mai daraja ba mai ƙwacen ƙasa ba ne, wanda ke kwaɗayin kayan ɗan'uwansa. Wannan roƙon da ya yi da zuciya ɗaya

watakila ya shafi mutane ne fiye da kasa. Watakila yana rokon fadada iyakar yankinsa ne cikin salama don ta dauki karin mutane masu bauta wa Allah na gaskiya.

Na biyu, Jabez ya roki "hannun" Allah ya kasance da shi. Hannun Allah na alama shi ne ikon da yake nunawa, wanda yake amfani da shi ya taimaki masu bauta masa. (1 Labarbaru 29:12) Don ya samu bukatun da ke zuciyarsa, Jabez ya dogara da Allahn da hannunsa bai gajarta ba ga wadanda suka yi imani da shi.—Ishaya 59:1.

Na uku, Jabez ya yi add'ua: 'Ka kiyaye ni daga mugunta, kada ta ciwuce ni!' Furcin nan "kada ta ciwuce ni" mai yiwuwa yana nufin cewa Jabez ya yi addu'a ne, ba don ya tsira daga bala'i ba, amma domin ya kauce wa yin bakin ciki ko kuma sakamakon mugunta ya sha kansa.

Addu'ar Jabez ta nuna yadda ya damu da bauta ta gaskiya da kuma bangaskiyarsa da dogararsa ga Mai jin addu'a. Mene ne Jehobah ya yi? Wannan gajeren labarin ya kammala da kalmomin nan: "Allah fa ya yarda masa da abin da ya roka."

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

_w05_ 10/1 29 sakin layi na 7
Darussa Daga Littafin Tarihi na Daya

5:10, 18-22. A kwanakin Sarki Saul, kabilun da suke gabashin Urdun sun ci Hagarawa a yaki duk da yake cewa Hagarawan sun ninka su sau biyu a yawa. Hakan ya faru ne domin jaruman wadannan kabilun sun dogara ga Jehobah kuma sun nemi taimakonsa. Bari mu dogara ga Jehobah yayin da muke ci gaba da yaki na ruhaniya da makiyanmu da suka fi mu yawa.—Afisawa 6: 10-17.

30 GA JANAIRU–5 GA FABRAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 1 TARIHI 7-9

"Da Taimakon Jehobah, Za Ka Iya Aikin da Ya Ba Ka"

_w05_ 10/1 29 sakin layi na 8
Darussa Daga Littafin Tarihi na Daya

9:26, 27. Lawiyawa masu tsare kofa suna da matsayi na rikon amana. An ba su makullin bude hanyar wuri mai tsarki na haikalin. Sune suke bude ta kowace rana. An ba mu hakkin nemo mutane a yankinmu kuma mu taimake su su zo su bauta wa Jehobah. Bai kamata a dogara kuma a amince da mu kamar yadda aka amince da Lawiyawa masu tsare kofa ba?

_w11_ 9/15 32 sakin layi na 7
Shin Za Ka Iya Zama Kamar Finehas Sa'ad da Ka Fuskanci Kalubale?

Finehas yana da hakki mai girma a Isra'ila ta dā, amma da gaba gadi da basira da kuma dogara ga Allah, ya yi nasara duk da yanayi mai wuya. Kuma Jehobah ya amince da yadda Finehas ya kula da ikilisiyar Allah da kwazo. Bayan shekaru 1,000, an hure Ezra ya rubuta: Finehas "dan Eleazar shi ne mai-mulkinsu a kwanakin dā, Ubangiji kuwa yana tare da shi." (1 Laba. 9:20) Bari ya kasance hakan ga dukan wadanda suke shugabanci tsakanin mutanen Allah a yau, hakika, ga dukan Kiristoci da suke bauta masa da aminci.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

_w10_ 12/15 21 sakin layi na 6
Ka Rera Waka Ga Jehobah!

6 Hakika, ta wurin annabawansa Jehobah ya umurci masu bauta masa su yabe shi da

waƙa. An cire mawaƙa daga yin hidimomi da wasu Lawiyawa suke bukatan su yi domin su ba da isashen lokaci ga rubuta da kuma gwada waƙoƙin.—1 Laba. 9:33.

6-12 GA FABRAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 1 TARIHI 10-12

"Ku Ci-gaba da Son Yin Nufin Jehobah"

***w12* 11/15 6 sakin layi na 12-13**
'Ka Koya Mini Na Aikata Nufinka'

12 Dauda misali ne mai kyau na wanda ya bi ƙa'idodin da ke cikin kalmar Allah a rayuwarsa. Ga wani misali. Wata rana, Dauda ya ji ƙishirwa sosai kuma ya ce yana son ya sha ruwa "daga rijiyar Baitalahmi." A lokacin, Filistiyawa ne suka mallaki wannan birnin. Sai sojojinsa uku suka shiga birnin a bakin ransu kuma suka ɗebo masa ruwa. Amma Dauda ya ƙi sha, kuma "ya tsiyaye shi a gaban Ubangiji." Me ya sa? Dauda ya ce: "Allahna ya tsare ni da in yi wannan: zan sha jinin waɗannan mutane, da suka kasaidda ransu? gama da hatsarin ransu suka kawo shi." —1 Laba. 11:15-19.

13 Dauda ya san cewa dokar Jehobah ta ce kada a ci jini, amma a zubar a ƙasa. Kuma ya fahimci abin da ya sa dokar ta ce a yi hakan. Dokar ta ce "ran nama yana cikin jini." Amma fa, me ya sa Dauda ya ƙi sha tun da ruwa ne? Domin ya san ƙa'idar da ke tattare da dokar da aka bayar game da jini. Ya koyi cewa jini abu ne mai daraja a gaban Jehobah. Kuma ya san cewa waɗannan sojojin sun saka rayukansu cikin haɗari ne don su ɗebo ruwan. Saboda haka, Dauda ya zubar da ruwan a ƙasa.—Lev. 17:11; K. Sha 12: 23, 24.

***w18.06* 17 sakin layi na 5-6**
Ka Bar Dokokin Allah da Kuma Ka'idodinsa Su Ja-gorance Ka

5 Idan muna son dokokin Allah su taimaka mana, ba karanta Littafi Mai Tsarki kaɗai za mu riƙa yi ba. Dole ne mu ƙaunace dokokin Allah kuma mu daraja su. Kalmar Allah ta ce: "Ku ƙi mugunta, ku so abu mai kyau." (Amos 5:15) Amma ta yaya za mu iya yin hakan? Ya kamata mu riƙa ɗaukan abubuwa yadda Jehobah yake ɗaukan su. Alal misali: A ce kana fama da rashin barci. Sai ka je asibiti kuma likita ya gaya maka irin abincin da za ka riƙa ci da irin motsa jikin da za ka riƙa yi. Kari ga haka, ya gaya maka cewa ka daina yin wasu abubuwan da ka saba yi. Sa'ad da ka dawo gida, sai ka yi su kuma ka lura cewa sun taimaka maka! Babu shakka, za ka yi farin ciki sosai domin likitan ya taimaka maka ka magance matsalarka.

6 Hakazalika, Mahaliccinmu ya ba mu dokokin da za su kāre mu daga fuskantar sakamako marar kyau na yin zunubi kuma za su sa mu kyautata rayuwarmu. Alal misali, Littafi Mai Tsarki ya ce kada mu riƙa yin ƙarya da zamba da sata da lalata da mugunta da kuma sihiri. **(Karanta Karin Magana 6:16-19;** R. Yar. 21:8) Idan mun lura cewa muna amfana sosai daga bin dokokin Jehobah, hakan zai motsa mu mu ƙaunace shi da kuma dokokinsa.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

***it*-1-E 1058 sakin layi na 5-6**
Heart

Serving With "a Complete Heart." The literal heart must be whole to function normally, but the figurative heart can be divided. David prayed: *"Unify my heart* to fear your name," suggesting that a person's heart could be divided with regard to its affections

and fears. (Ps 86:11) Such a person may be "halfhearted"—lukewarmly worshiping God. (Ps 119:113; Re 3:16) An individual can also be of "a double heart" (literally, with a heart and a heart), trying to serve two masters, or deceptively saying one thing while thinking something else. (1Ch 12:33; Ps 12:2, ftn) Jesus strongly denounced such doublehearted hypocrisy.—Mt 15:7, 8.

One seeking to please God must be neither halfhearted nor doublehearted but must serve him with a *complete* heart. (1Ch 28:9) This requires diligent effort in view of the heart's being desperate and inclined to badness. (Jer 17:9, 10; Ge 8:21) Of help in maintaining a complete heart are: heartfelt prayer (Ps 119:145; La 3:41), regular study of God's Word (Ezr 7:10; Pr 15:28), zealous participation in preaching the good news (compare Jer 20:9), and association with others whose hearts are complete toward Jehovah.—Compare 2Ki 10:15, 16.

13-19 GA FABRAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 1 TARIHI 13-16

"Bin Umurni Yakan Sa Mu Yi Nasara"

w03 5/1 16 sakin layi na 12
Kana Tambaya Kuwa, "Ina Ubangiji?"

12 Bayan da aka mayar da sunduƙin alkawari na Isra'ila kuma ya zauna na shekaru da yawa a Kiriath-jearim, Sarki Dauda ya so ya kai shi Urushalima. Ya nemi shawarar hakiman mutanen kuma ya ce za a ɗauki Sunduƙin 'idan sun yarda kuma idan zai gamshi Jehovah.' Amma bai bincika sosai ya tabbata nufin Jehovah game da batun ba. Da ya yi haka, da ba za a ɗora Sunduƙin bisa keken shanu ba. Da Kohatawa na Lawi sun ɗauka a kafaɗarsu, yadda Allah ya bayyana sarai. Ko da yake sau da sau Dauda yana biɗan Jehovah, a wannan lokaci ya kasa yin haka a hanyar da ta dace. Sakamakon ya zama bala'i. Daga baya, Dauda ya fahimci cewa: "Ubangiji, ya auko mana, da shi ke ba mu neme shi bisa ga ƙa'ida ba."—1 Labarbaru 13:1-3; 15:11-13; Litafin Lissafi 4:4-6, 15; 7:1-9.

w03 5/1 16-17 sakin layi na 13
Kana Tambaya Kuwa, "Ina Ubangiji?"

13 A ƙarshe da Lawiyawa suka ɗauki Sunduƙin daga gidan Obed-edom zuwa Urushalima, Dauda ya shirya waƙa da aka rera. Ya haɗa da tunasarwa mai kyau: "Ku biɗi Ubangiji da ikonsa; Ku biɗi fuskatasa tuttur. Ku tuna da ayyukan da ya yi na ban mamaki; al'ajabansa kuma, da shari'un bakinsa."—1 Labarbaru 16:11, 12.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

w14 1/15 10 sakin layi na 14
Ka Bauta wa Jehobah, Sarkin Zamanai

14 Dauda ya kawo sunduƙin alkawari cikin Urushalima. A wannan lokaci na farin ciki, Lawiyawa sun rera wata waƙar yabo da ke ɗauke da wasu kalmomi masu muhimmanci da ke littafin 1 Labarbaru 16:31. Ayar ta ce: "A cikin al'ummai kuma ku ce, Ubangiji yana mulki ['Jehobah ya zama Sarki!' *NW*]" Wani zai iya yin tunani cewa, 'Tun da Jehobah ne Sarkin zamanai, me ya sa aka ce ya zama Sarki a wannan lokacin?' Jehobah ya zama Sarki sa'ad da ya yi amfani da ikonsa ko kuma ya naɗa wani ya wakilce shi. Yana da muhimmanci mu fahimci yadda Jehobah ya zama Sarki. Kafin Dauda ya mutu, Jehobah ya yi masa alkawari cewa sarautarsa za ta ci gaba har abada, ya ce: "Zan kafa zuriyarka daga bayanka, wanda za ya fito daga tsatsonka, zan kuma kafa mulkinsa." (2 Sam. 7:

12, 13) Wannan alkawarin ya cika sa'ad da ‘zuriya’ ko kuma ɗan Dauda ya bayyana bayan shekaru fiye da 1,000. Wane ne wannan ɗan, kuma a yaushe ne ya zama Sarki?

20-26 GA FABRAIRU

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 1 TARIHI 17-19

“Ka Ci-gaba da Farin Ciki a Duk Yanayi da Ka Sami Kanka”

***w06* 8/1 7 sakin layi na 1**
Ka Mai Da Hankali Ga Alherin Kungiyar Jehobah

DAUDA na Isra'ila ta dā yana cikin fitattun mutanen da aka ambata a Nassosin Ibrananci. Wannan makiyayi, mawaƙi, annabi, da kuma sarki ya dogara ga Jehobah Allah ƙwarai. Dangantakar Dauda na kud da kud da Jehobah ya sa shi ya so ya gina wa Allah gida. Gidan nan ko kuma haikali, zai zama cibiyar bauta ta gaskiya a Isra'ila. Dauda ya san cewa tsari na haikalin zai kawo farin ciki da albarka ga mutanen Allah. Shi ya sa Dauda ya rera waƙa cewa: “Mai-albarka ne mutum wanda ka [Jehobah] zaɓa, wanda ka ke sa shi gusa gareka, domin shi zauna cikin gidajenka: Ranmu za ya kwanta da alherin gidanka, wuri mai-tsarki na haikalinka ke nan.”—Zabura 65:4.

***w21.08* 22-23 sakin layi na 11**
Ka Yi Farin Ciki don Ayyukan da Kake Yi a Kungiyar Jehobah

11 Mu ma za mu iya daɗa yin farin ciki idan muka yi ***iya ƙoƙarinmu*** wajen yin aikin da aka ba mu a ƙungiyar Jehobah. Ka yi ƙwazo sosai a wa'azi, kuma ka yi aiki tuƙuru a ikilisiya. (A. M. 18:5; Ibran. 10:24, 25) Ka yi shiri da kyau don ka iya ba da kalamai masu ban ƙarfafa a taro. Ka ɗauki kowane jawabi da aka ba ka a taron tsakiyar mako da muhimmanci. Idan an ba ka aikin yi a ikilisiya, ka riƙa zuwa taro da wuri. Kada ka ɗauka cewa ka fi ƙarfin aikin da aka ba ka. Ka yi ƙoƙari ka koyi aikinka da kyau. (K. Mag. 22:29) Idan ka yi aiki da ƙwazo a ikilisiya, za ka ƙarfafa dangantakarka da Jehobah kuma za ka yi farin ciki. (Gal. 6:4) Kari ga haka, zai yi maka sauƙi ka yi farin ciki idan aka ba wasu aikin da kake so a ba ka.—Rom. 12:15; Gal. 5:26.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

***w20.02* 12, akwati**
Muna Kaunar Jehobah, Ubanmu Sosai

Jehobah Ya San da Ni Kuwa?
Ka taɓa yi wa kanka wannan tambayar: ‘Akwai biliyoyin mutane a duniya, Jehobah ya san da ni kuwa?’ Mutane da yawa sun yi irin wannan tambayar. Sarki Dauda ya rubuta cewa: “Ya Yahweh, mene ne mutum da har ka damu da shi? Ɗan Adam, da har kana tunaninsa?” (Zab. 144:3) Dauda yana da tabbaci cewa Jehobah ya san shi sosai. (1 Tar. 17:16-18) Ta Kalmarsa da kuma ƙungiyarsa, Jehobah ya tabbatar mana da cewa yana ganin yadda muke nuna cewa muna ƙaunar sa. Ka yi la'akari da wasu furuci a Kalmar Allah da suka tabbatar da hakan:

- Jehobah ya san ka tun kafin a haife ka. —**Zab. 139:16.**
- Jehobah ya san abin da ke zuciyarka, kuma ya san abin da kake tunani.—**1 Tar. 28:9.**
- Jehobah yana saurarar dukan addu'o'inka. —**Zab. 65:2.**
- Jehobah ya damu da dukan abubuwan da kake yi.—**K. Mag. 27:11.**
- Jehobah ne ya jawo ka gare shi.—**Yoh. 6:44.**

• Jehobah ya san ka sosai, kuma idan ka mutu, zai ta da kai. Zai ba ka sabon jiki da zuciya kamar wanda kake da shi a yanzu. Zai dawo maka da tunaninka da halayenka masu kyau.—**Yoh. 11:21-26, 39-44; A. M. 24:15.**

27 GA FABRAIRU–5 GA MARIS

DARUSSA DAGA KALMAR ALLAH | 1 TARIHI 20-22

"Ku Taimaka Wa Yara da Matasa Su Yi Nasara"

***w17.01* 29 sakin layi na 8**
"Ka Danƙa ma Mutane Masu-Aminci"

8 **Karanta 1 Labarbaru 22:5.** Wataƙila Dauda ya ga cewa wannan aikin ya fi ƙarfin Sulemanu. Me ya sa? Saboda haikalin "mai-daraja ƙwarai da gaske" ne, kuma a lokacin Sulemanu "ƙarami ne, yana kuwa da ƙuruciya." Amma Dauda ya san cewa Jehobah zai taimaka wa Sulemanu ya idar da aikin da ya ba shi. Don haka, Dauda ya mai da hankali ga abin da zai iya yi don ya taimaka, sai ya soma tattara kayan da za a yi aikin da su.

***w17.01* 29 sakin layi na 7**
"Ka Danƙa ma Mutane Masu-Aminci"

7 Babu shakka, Dauda ya so ya gina wa Jehobah haikali, wataƙila ya yi baƙin ciki sa'ad da aka gaya masa cewa ba shi ne zai yi hakan ba. Duk da haka, ya tallafa wa ɗansa Sulemanu. Dauda ya taimaka wajen shirya ma'aikata da za su riƙa tattara jan ƙarfe da azurfa da zinariya da kuma itace. Kuma ya ƙarfafa Sulemanu ya ce: "Yanzu fa, ɗana, Ubangiji shi zauna tare da kai; ka yi albarka, ka gina gidan Ubangiji Allahnka, kamar yadda ya ambata a kanka."—1 Laba. 22:11, 14-16.

***w18.03* 11-12 sakin layi na 14-15**
Iyaye, Kuna Taimaka wa Yaranku Su Yi Baftisma?

14 Dattawa za su iya tallafa wa iyaye yayin da suke ƙoƙarin taimaka wa yaransu. Za su iya yin hakan ta wajen ƙarfafa su su kafa maƙasudai a hidimar Jehobah. Wata 'yar'uwa ta tuna tattaunawar da ita da Ɗan'uwa Russell suka yi sa'ad da take 'yar shekara 6. Ta ce: "Ya ɗau minti 15 don ya tattauna da ni game da maƙasudaina a hidimar Jehobah." A sakamakon haka, ta soma hidimar majagaba kuma ta yi sama da shekaru 70 tana hidimar. Babu shakka, ƙarfafawa tana shafan rayuwar mutane sosai. (Mis. 25:11) Dattawa za su kuma iya ba iyaye da yaransu ayyuka a Majami'ar Mulki. Za su iya ba yaran ayyukan da za su iya yi dangane da shekarunsu.

15 Sauran 'yan'uwa a ikilisiya ma za su iya taimaka ta wajen nuna cewa sun damu da yara da kuma matasa. Za ku iya lura cewa wani yaro a cikin ikilisiya yana ƙarfafa dangantakarsa da Jehobah. Alal misali, wataƙila ya yi kalamai masu ban ƙarfafa a taro ko kuma ya yi aiki a taron tsakiyar mako. Ko ya fuskanci jarrabawa amma ya magance su. Ko ya yi wa'azi a makaranta sa'ad da ya sami zarafin yin hakan. Idan kun lura da haka, kada ku yi jinkirin yaba musu! Zai dace mu riƙa tattaunawa da yara da kuma matasa kafin a soma taro da kuma bayan an idar da taron. Idan muna yin hakan, yara za su ji cewa su ma suna cikin "babbar" ikilisiya.—Zab. 35:18.

Abubuwa Masu Daraja Daga Kalmar Allah

***w05* 10/1 31 sakin layi na 5**
Darussa Daga Littafin Tarihi na Daya

21:13-15. Jehobah ya umurci mala'ikan ya dakatar da annobar domin ba ya son ya ga mutanensa suna wahala. Hakika, "shi mai yawan jinƙai ne."

© 2022 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania